# SAMUWA DA HABBAKAR DIBBU A UNGUWAR KUSFA

**Isah BALA**

Kaduna State College of Education, Gidan Waya, Kafanchan, Nigeria
Corresponding Author: Isahbala1975@gmail.com; 07035141555

**Tsakure**

Wannan takarda mai taken Samuwa da ha~~akar [ibbu a Unguwar Kusfa Zaria. Manufar wannan bincike ita ce, a fito da tarihin Unguwa Kusfa da samuwa [ibbu da ha~akarsa an fito da gudunmuwar Malamanta ta fuskar samar da magungunan [ibbu da ayyukansu na malanta wanda suka taimaka wajen bun}asa al'adun Hausawa da Birnin Zariya gaba ]aya, bugu da }ari anyi amfani da kai ziyarar gani da ido domin tattaunawa da malaman [ibbu an Unguwar Kusfa da wa]anda suke tare da su a matsayin ginshi}iyar hanyar nemo bayanai ga wannan bincike. Binciken ya gano asalin Unguwar Kusfa ta kafune a sanadiyyar zuwan Malam Shitu [an Abdulrauf, ta kuma sami sunanta ne daga Kwasfa, wato magudanar ruwa. Binciken ya gano, ]ibbu ya samo asali ne a Kusfa, saboda zurfafa da Malaman suka yi akan ilimi sai a ]auki duk wata aya da tai munasaba da wani abu da ya ke cikin }ur'ani, sai a ce maga nin kazane. Bugu da }ari, binciken ya gano ire-iren taimako na magungunan waraka da Malaman ke bayarwa, dan gane da fannonin rayuwa maban-banta. A }arshe an bayar da wannan shawarwari sannan aka kamala sai manazarta.

## 1.1 Gabartawa

Tun farkon tarihin Hausawa }asar Hausa a cike take da masu bayar da magani don warkar da cututtuka ana cikin haka ne sai Addinin Musulunci ya shigo }asar Hausa wanda al'ummar Hausawa suka kar~eshi hannu biyu-biyu, wannan ta samarwa al'ummar Hausawa wata sabuwar hanyar magunguna ta ]ibbu wato hanyar yin amfani da addu'oin da rubutu ha]i da itatuwa wajen neman waraka shi kuwa magani ta hanyar ]ibbu yana }unshe ne da tarin hanyoyi da ilimai masu yawa da malamai ke amfani da su domin biyan bu}atun al'umma.

## 2.1 Ta}aitaccen Tarihin Unguwar Kusfa:

Kusfa wata Unguwa ce a cikin garin Zariya, da ke Jahar Kadunan Najeriya. Ta wajen gari wato bayan ganuwa, ta kama tun daga Kofar Gayan zuwa Kofar Kuyambana. Ta cikin gari daga Kofar Kuyambana zuwa kasuwa har zuwa Kofar Gayan. Tana Yamma maso kudu a cikin gari, tana da kimanin murabba'in kilo mita biyar zuwa shida. (Hira da Sa'idu a ranar (15/7/2019).

Asalin mutanen gidan Fulani da ke Unguwar Kusfa ta Zariya, sun taso ne daga }asar Futa-toro wato, daga can }asar (Mali) ta yanzu suka ~ullo ta }asar Nijar suka biyo ta Sokkwato suka zo Zariya, fiye da shekara ]ari bakwai. Hira damuka yi da Malam Lawal Maiwada (2019), ya bayyana cewa:

Wannan }ungiya na Fulani, sun zo Kusfa ne a lokacin ba ta da suna. Sun iske Unguwar babu wani gida duk wurin daji ne, sai fadamu da shuke-shuken ganyaye., suka kafa bukkokinsu guda uku. Daga cikin wa]anda suka zo akwai Malam Ja~~o da Malam Muhammadu, wanda shi ne jagoran tafiya tare da shanunsu.Wa]ansu daga cikin Fulanin sun wuce zuwa Karau-karau, wasu suka wuce zuwa Igabi. Sunkafa garin daga nan ne suka ya]u wasu zuwa Kagarko, suna noma da kiwo.

Kamar yadda tarihi ya nuna daga bakin masana Unguwar Kusfa, gidan Fulani, shi ne gida na farko da aka fara samu, wanda sun zo ne daga }asar Mali wato Futa-toro. Sun kafa bubkoki, a lokacin Unguwar babu kowa sai itatuwa da fadamu. Bayannan sai zuwan Malam Shitu [an Abdulra'uf da yayansa Malam Yusuf wa]anda asalinsu Larabawa daga }asar Tunisia, sunzo Zaria ne a zamanin Sarkin Zazzau Abdulkarimu sarki na uku a daular Usmaniyya, Malam Shitu ya tafi yamma da gari kusa da wata rigar Fulani kuma kusa da wani Kududdufi ya gina gidan sa sunan da ake kiran wannan kududdufi shine Kwasfa wato magudanar ruwa daga nan ne Anguwar Kusfa ta samo sunanta.

## 2.2. Samuwar [ibbu a Unguwar Kusfa

[ibbu ya samo asali a Kusfa ne, saboda zurfafa da malaman suka yi a kan ilimi. Kamar yadda ya zo a cikin Nafsi cewa, ilimi iri biyu ne wato, (العلم علمان علم الفقه للديان وعلم طب للبدان) ilimin Fi}ihu domin sanin addini

yadda za a bautawa Allah. Sai kuma, ilimin magunguna yanda za a kare jukkuna, to wannan Nafsi shi ne babbar hujjar malaman Kusfa na ri}e ilimin [ibbu, wato ilimin sanin magunguna. A dalilin karatun }ur'ani da aka yi ta haka ne ake ]aukar duk wata aya da tayi manasaba da wata abu da yake cikin }ur'ani, sai ace wannan maganin kazane ta hanyar jarabawa. Kamar yadda Malam Suyu]i ya shaida mini cewa, a ranar 1/1/2023 Malam Musan Wa'alamu yana cikin wa]anda suka fara bayar da magungunan ]ibbu, ta hanyar ha]a itace da rubutu asha a yi wanka.

**3.1 Ma'anar [ibbu**

{amusun Hausa (2006) ya bayyana ma'anar [ibbu da cewa, magani ta yin rubutun sha ko duba ko surkulle.

{amusun Larabci (1972) ya bayyana ma'anar Kalmar da cewa, shi ne maganin jiki ko zucciya.

[ibbu – Kalma ce ta Larabci da ke nufin "Magani". Malaman Kusfa suna tafi da harkar ]ibbunsu ne ta hanyar amfani da abin da ya zo a Hadisan Manzon Allah(S.A.W), da kuma ri}on littafai na magabata da sukai bincike akan abin da ya shafi ]ibbu. Ga malaman kamar haka:

i. Malam Sidi Dogara
ii. Malam Adam Sa'idu
iii. Malam Yunusa Abubakar
iv. Malam Hussaini [alibi
v. Malam Muntari Tanimu Akibiya
vi. Malam Aliyu Abdulrahman
vii. Malam Aliyu [ansidi
viii. Malam Suyu]I Abubakar
ix. Malam Aliyu Suleiman
x. Malam Garba Sani
xi. Malam Safawanu Mansur
xii. Malam Salihu Muhammadu
xiii. Malam Yusuf Lawal
xiv. Malama 'Yarinna

4.1 Littafan [ibbu

Ga ka]an daga cikin littafan da malaman Kusfa suka yi ri}o da su, kuma suke tafi da shi wajen harkar [ibbunsu, kamar haka:

1. Littafin [ibbun Nabi(طب النبي)

   Wannan littafi Imamu Ibini {ayyum Aljauziyya ya rubuta, wanda babu abin da ke ciki sai bayanin magunguna.

2. Littafin Arrahamatu fi [ibbi Walhikima (الرحمة في طب والحكمة)

   Wannan littafi Jalaluldini Suyi]i ya rubuta, wanda akwai bayanin magunguna.

3. LittafinAlgazalilkabirfil'ilajatiArrahaniyya (الغرا لكبير في العلاجات الروحانية)

   Wannan littafi Imamu Abuhamid Algazali ya rubuta, a ciki akwai magana akan magani.

4. LittafinMujarrabatu(مجربات)

   Wannan littafi Imamu Muhuyiddini Ibinil Arabi ya rubuta, wanda a ciki akwai bayanin magunguna.

5. Littafin Al}anunu Fi]]ibbi(القانون في الطب)

   Wannan littafi Ibini Sina ya rubuta, babuabin da keciki sai bayanin magunguna.

**5.1 Ma'anar Magani**

Bunza, (1990) Ya yi bayanin magani da cewa, magani shi ne yin amfani da duk wata hanya da za ta warkar ko kwantar ko rage wata cuta ta ciki ko ta waje wadda aka samu ta ha]ari ko kuma neman kariya ga cuta ko

abokan hamayya ko neman ]aukaka da daraja ko ta buwaya ta hanyar Siddabaru da Sihirce-Sihirce na ban al'ajabi.

Ahmad, (1984) Magani shi ne, duk wani abu da za a yi, ko wata hanya, ko kuma wata dabara da ake yi don gusar da wata cuta daga jikin mutum ]ungurumgum, ko kuma kwantar da ita don kawo jin da]i ga jiki ko ga zuciya don sauwa}e duk wahala da damuwa da ita cutar kan iya haifar.

Sarki, (2011) ya ce, waraka waninau'inimani ne da ya danganci magani da ake tanada da cututtuka da ake iya gani a jikin mutum.

Magani na nufin }o}arinkawarda cuta kowace iri daga jikin mai fama da ita, ko kwantar da ita, ko kuma neman kariya daga kamuwa da cuta, ko kuma neman gwada bajinta da kwazo da ]aukaka da daraja a idon mutane ta hanyar Sihirce-Sihirce.

Waraka na nufin duk wani abu da za a yi na magani domin samun lafiya daga cutan da ke jikin ]an Adam.

Akwai taimako da Malaman Kusfa kan bayar, idan wata matsala ta samu mutum, don neman waraka. Idan an kai kuka ga Malaman. Ka]an daga cikin magungunan taimako sun ha]a da:

5.2 Magungunan [ibbun da Malaman Kusfa ke Bayarwa


Bu}atun Neman Aure

Funtua. (2010;64)cewaya yi, aure yarjejeniya ne tsakanin mace da namiji bisa }a'idoji na addini ko na al'ada.

{amusun Hausa (2006) ya ba da ma'anar aure da cewa, shi ne dangantaka tsakanin namiji da mace ta hanyar shari'a. Ya }ara da ba da ma'anarha]a wani tsira da wani tsiro don samuningantacceniri.

Idan mace na neman aure, malaman Kusfa kan bayar da taimako don samun nasara ga mai nema. Irin taimakon da malaman kan bayar sun ha]a da:

1.بسم الله الرحمن الرحيم



Wannan Hatimi fa'ida ce da kan kawo wa mace masoya matu}a da farinjini matu}ar tana amfani da shi. A rubuta wannan Hatimi ga macen da ke neman aure ko miji, sai a yi Laya tarataya a jikinta,da zarar ta aiwatar da haka, to kuwa nan da nan za ta ga masoya na ketowa daga ko'ina, suna zuwa wajenta. Yawanci ana bayar da shi ne ga mace mai neman mijin aure da masoya cikin gaggawa.

**2. Ayoyin {ur'ani**

Akan yi amfani da suratul Yasin ko Fatiha wajen daidaita yuwuwar aure ko in ya ~aci a gyara. A karanta }afa ]aya, amma akwai abin da za'a karanta in an zo Mubin sai a karanta Fatiha }afa bakwai.

3. **Wuridi**

**Alamnasharaha**

**Ayatul Kursiyyu**

Wa]annan ayoyi akan bayar da su ne, ga samari ko budare masu neman mata ko miji. Yadda ake aiwatarwa shi ne, mai neman zai yi Alwala ne ya yi Salla nafila raka'a biyu. Zai karanta abin da ya sauwa}a na {ur'ani. Yayin da ya kamala, sai ya karanta ayatul kursiyyu }afa hamsin (50) da suratul Alamnasharaha, har zuwa }arshen sura ita ma }afa hamsin. Idan ya gama, sai ya karanta wannan addu'ar yana cewa:

Ya Allah ina baka za~i da saninka, ina neman gafararka da ikonka, ina ro}onka da falalanka mai girma. Ya Allah don kai kake da iko, ni ba ni da iko, kai ka sani ni ko, ban sani ba, kai ne Sarki masanin fake. Ya Allah in ka san wannan al'amari da nake nema da wannan aure, sai a fa]i sunan wanda ake nema a nan.idanalherine gare ni, a cikin addinina da duniyana da rayuwana da }arken al'amarina ka }addara mini wannan aure. Kuma ya Allah, ka sauwa}e mini shi, ka sa mini albarka a cikinsa. Allah in ka san neman auren da nake yi na wance, sheri ne gare ni a cikin addinina da duniyana da rayuwana da }arken al'amarina, ka juyar da al'amarin ga barina ka juyar da abin gare ni, ka }addara mini alheri, duk inda yake. Kuma ka yarda dani da alheri. Sai a yi wa Annabi Salatiashafa, a yi har sau uku.

**Haihuwa**

1. Hatimi




A rubuta wa macen da ke bi]ar haihuwa, sai a sami sassa}en ~aure da nonon kurciya a dake su wuri ]aya. Sannan a sa shi cikin mahaifar kaza, su bushe tare a dake su. Sannan kuma matar ta ci har kwana bakwai, a fara ranar Lahadi zuwa Asabar tare da wannan aya da ke sama}afa ashirin da ]aya.

**2. Ayoyin {ur'ani**

A rubuta Suratul Anbiya'i da Suratul Yusuf don neman haihuwa, har ya zuwa }arshen sурorin a sha. Insha Allahu za a sami haihuwa.

**3. Wurudi**

رب لا تزني فردا وأنت خيرالواريثن

A yi wurudin wannan Ayar dubu ]aya da ]ari ]aya da goma sha ]aya kwana bakwai. In Allah ya so za a sami haihuwa.

Goyon Ciki

Goyan ciki, al'ada ce da Hausawa suke yi mata musamman masu cikin fari. Idan ta sami ciki har ya kai watanni, za ta tafi gidansu ta zauna. A wannan lokaci, duk wani abu na magani da zai taimaka ta sauka lafiya kuma ya kare ta da abin da ke cikinta, za a nemo a ba ta. Akan zagara nema, tun daga rubutu ko ji}o ko sassa}e da abin da zai taimaka.

**1. Ayoyin {ur'ani**

قل هوالله احد
قل أعوب برر الغلق
قل أعوب برب الناس
الله لا إلله الاهو الحى الفيوم

Za a rubuta wa]annan surorin ne }afa uku-uku, wato sau uku-uku sai a rubuta Salatin Annabi (S.A.W), shi ma }afa uku. Za a wanke a bata ta sha, idan ana yi mata haka kullum, to kuwa za ta sami goyan ciki, cikin nasara har ya zuwa na}uda.

سورة الحاقة
"الحاقة ماالحاقة ، ومالدرك ماالحاقة"

Idan mace na goyon ciki, wannan surar tana daga cikin taimakon da Malaman Kusfa sukan bayar wanda za a rubuta surar sukutun a wanke da ruwa, idan so samu ne ma a sa ruwan Zamzan ne a ri}a ba ta tana sha. Kuma kullum za a ri}a yin mata tsawon lokacin goyan cikinta.

**2. Wurudi**

" يا كافي، ياغني، يافتاح، يا رزاق"

Ana wurudi, wa]annanayoyi}afa dubu ]aya da ]ari ]aya da goma sha ]aya ga mace mai goyon ciki, da yardar Allah za'a yi goyon ciki lafiya.

الله لطيف


A yi wurudin, wannan sunan Allah }afa ]ari uku da goma sha uku, ga mace mai goyon ciki. Za ta yi goyoncikin lafiya, da yardar Allah.

Na}uda

{amusun Hausa ( 2006) ya bayyana ma'anarNa}uda da cewa, ciwon da mace take yi dab da haihuwa.

Na}uda wani hali ne da mace mai ciki takan shi ga, a lokacin da take gab da ta haifi abin da ke cikin cikinta. Yayin da mai ciki ta shiga wannan hali, akwai taimakon da akan taimaka mata da shi, domin ganin ta haifi abin da ke cikin nan nata lami lafiya. A nan ma ba a bar Malaman Kusfa a baya ba. Don kuwa akwai irin taimakon da sukan bayar a wannan hali da suka ha]a da:

1. **Hatimi**



A rubuta wannan hatimi }afa bakwai bayan ciki ya kai wata bakwai, insha Allahu za ta haihu lafiya ba tare da wata matsala ba.

**2. Ayoyin }ur'ani**

بسم الله الرحمن الرحيم

Wannan ita ce mabu]in kowace Sura daga cikin Surorin Al-}ur'ani. Za a rubuta ne sau goma sha ]aya(11) sai a rubuta sunan Allah"Ya Allahu" }afa sittin da shida ( 66), sai a wanke a ba ta ta sha. Da izinin Allah da zarar an yi haka, za a kai ga }arshen wannan dogon na}udar, wato za ta haihu cikin sau}i.

أ. لاحول ولاقوة الابالله العلى.

ب. يحرج من بين سب.

1. Arubutawannanaya"**Lahaula Wala {uwwati Illa Billa**" }afa goma sha ]aya (11), sai "**Yakharuju Min Baini Sulbi**" . Ita ma wannan ayar sau goma sha ]aya (11), sai a wanke rubutun, a ba ta ta sha. In Allah Ya yarda za a haihu, ba tare da ~ata lokaci ba, ba za a yi tsawon na}uda ba.

2 **Salamun {aulan Minrabbi Rahim**

سلامقولامون من رب رحيم

Wannan aya ce daga cikin Al-}ur'ani mai girma. Za a rubuta ne }afa bakwai (7), sai a ha]a da Karkashi a ba ta, ta sha. Da yardan Allah idan an yi haka, za a haifi cikin nan lafiya ba tare da samun tangar]a ba.

3. **Wurudi**


يا سلام سلم

A yi wurudin wannan sunan Allah }afa dubu, in kuma na}udar ya taso ne a yi ta karantawa ba adadi.

Karatu

Fahami na ]aya daga cikin manyan magunguna da malaman Kusfa ke ba da wa ga al'umma, musamman idan aka sami yara wa]anda suke da }arancin fikira na ]aukan karatu. Don haka, karatu na da matu}ar muhimmanci a al'ummar }asar Hausa saboda haka, a duk lokacin da yakasance yaro ko yarinya suna da sha'awar karatu, sannan kuma suna da }arancin fahimta ko yawan mantuwa. Akan garzaya zuwa wajen Malaman Kusfa su bayar da taimako.Wa]annan taimakon da sukan bayar galibi ayoyi ne na Al-}ur'ani kamarhaka:

1. Hatimi



Maganin Karatu, a rubuta wannan hatimi a sha tare da gya]a da yardar Allah za a sami karatu .

**2. Ayoyin {ur'ani**

**Arrahman Allamal {ur'an Khala}al Insan Allamahul Bayan**

"الرحمن علم الفرءنخلق الإنسان علمه البيان"

Za a rubuta wa]annan ayoyi ne a allo, }afa arba'in da ]aya (41), sai a sami sassa}en rimi ta ~angaren gabas. Bayan nan, sai a wanke rubutun, a saka sassa}en a cikin rubutun a juye shi ya kwana, sannan asha. Idan da hali akan so a sanya zuma a ciki lokacin da za a sha. Idan an yi wa yaro haka da izinin Allah }wa}walwarsaza ta bu]e ya sami karatu.

**Wa Allamaka Malam Takun Ta'alamWa Kana FadllahiAzima**

وألمنه مالم تكن تعلم وكن فلل الله علك عظيم.

Ana rubutawane a allo }afaarba'in da ]aya (41), sai a wanke rubutun, a barba]a lalli ka]an a sanya zuma farar sa}a, sai a ajiye. Da zarar alfijir ya keto, sai a sha ana tashi daga bacci ba tare da an wanke baki ba. Matu}ar aka ri}a yi wa yaro ko yarinya haka, to kuwa }wa}walwarsa za ta ha~aka karatu zai zauna da yardarm Allah.

بسم الله الرحمن الرحيم

سنغرئک فلاتنسی

**Sanu}uri'uka Fala Tansa**

Watan nan aya ce daga cikin {ur'ani, za a rubuta wannan aya }afa ]ari (100), a allo sai a wanke a ha]a da zuma ko a sami ruwan Zamzam, a ha]a maimakon zuma, sai a wanke rubutun da shi, sai a shanye nan take. Wannan idan ana yi wa yaro ko yarinya, to duk abin da suka karanta ba za su manta ba da yardar Allah.

**3. Wurudi**

رب زدنى علم وفحمل قرآن يارب العلمين

A yi wurudin wannan sunan Allah Rabbi ziddini ilman wa fahamil }ur'ani wal-ilmi ya rabbil Alamin }afa dubu har sati ]aya, da yardar Allah za a sami karatu.

MagungunanBu}atunZuciya

Wannanrukuni ya shafi magungunan da akan bayar ko akan nema don biyan bu}atar rayuwa, kotaimaka wa rayuwa ta gudana yadda ake bu}ata. Misali: Asiran neman aure mace ta so namiji da na farin jinni, da na kiran kasuwa da na neman mallaka, da na neman mulki ko ]aukaka da sauransu (Abdullahi, 2020).

Tsari

{amusunHausa(2006) ya bayyana ma'anar tsari da cewa,yin amfani da wani abu don kange wani abu.

Tsari shi ne neman dafa'i ko, kuma a ce garkuwa da ]an Adam kan nema don gujewa cutuwa daga abokan gabarsa.

Kamar yadda aka sani cewa, rayuwa cike take da gwagwarmaya, kuma da }alubale da sukan taso wa mutum. Wannan ya sa dole ne mutum ya nemi tsari daga abubuwan da za su illata shi ko lalata masa al'amari. Haka kuma, Bahaushe musamman Musulmi ya yi imani da cewa malamai suna da irin gudunmawar da za su iya bayarwa gare shi dangane da wani abu na rayuwarsa. Wannan ya sa akan le}a malaman Kusfa kuma sukan bayar da gudunmawa wajen neman kariya da suka ha]a da:

1. Hatimi



Maganin tsari a rubuta }afa ]aya ko hu]u ga yaro ko babba kwana bakwai ko hu]u a sha da yardar Allah za a sami kiyayewa.

**2. Ayoyin {ur'ani**

لقدجاء كم رسول من أنعبسكم عزيز عليه ماعننتم حريص
عليكم بالمومنين رءف رحيم فإن تولوا فقل حسبى الله لا إللهالاهوعليه توكلت وهورب العرش
العظيم.
الله لا إلاهوالحعى القيوم -:- ذوقرش.
لإيلف قريش ذوقرش
قل أعودب برب الغلق، ذوقرش
قل أعودب برب الناس، ذوقرش

A rubuta wa]annan ayoyin }afa ]ai-]ai, sai a wanke a ha]a da tsakin kuka, sai mutum ya sha ya yi wanka, in Allah Ya so Allah zai kare shi ga dukkan sharri da jifa.

3. **Wurudi**

حسبنا الله ونعم وكيل

A yi wurudin Hasbunallahu wani'imal wakeel }afa ]ari hu]u da hamsin a kullum bayan sallar subahi, da izinin Allah, Allah zai tsare.

**Hatimi**

**Ma'anar Hatimi**

Hatimi, wani zane ne da ake yimai }usurwa hu]u, kuma a bi shi da wasu }ananan layuka a kwance da tsaye, amma da shara]in kasancewarsu daidai wadaita, ba tare da wasu layukan na tsaye ko na kwance sun zarce wasu ba. Amma da shara]in kada adadin wani gida ya zarce na wani a yawa ko kuma a sami maimaituwa. (Al-Boney 1942:83).

Wannan Hatimi da ke sama, za a rubuta ne a allo }afa ]aya. Kuma a zana shi yadda yake, sai a sami kwano da ruwa mai kyau a wanke a ba mutum ya sha. Wannan fa'ida matu}ar mutum yana amfani da ita, to kuwa zai sami kariya daga sammu da jifa da yardar Allah, a wanke a ha]a da kaucin tsamiya a ba mutum ya yi wanka da shi, ya rataya layar a jikinsa. Za a sami kariya da yardar Allah, kuma duk wanda ya nufe ka da sharri, to zai koma masa har wanda ma ya kai hannu ya buge shi, zai iya rasa ransa.

Kafi


{amusun Hausa (2006) ya bayyana ma'anar kafi da cewa, layu da magunguna da ake birne wa don tsare gari ko gida ko mace ko wani abu.

Kafi na nufin yin magani don tsare gida daga sherin mayagu da ma shai]anu Aljanu.

Akwaiabubuwada MalamanKusfakan bayar domin kafi na muhalli, ko ]aki ko na wani abu kamar haka:

1. Hatimi

بسم الله الرحمن الرحيم.



Wananan hatimi, shi ma Sirri ne na kafin gida. Za a rubuta shi ne a fallen takarda a yi laya, sai a sami }ahon rago a saka shi a ciki, sai a birne a cikin gida. Wannan gida da yardar Allah ya kafu, sannan ~arayi ba za su iya shigaba. Idan kuwa har ya shiga, to da kan shi zai fito, ba tare da ya iya ]aukar ko tsinke ba daga wannan gida ba. Wannan sirrine mai fa'ida.

**2. Ayoyin {ur'ani**

A karanta Ayatul }ursiyyu }afa tara ana kewaye kowani }usurwa na gidan, da izinin Allah gida zai kafu, ba tare da wani abu ya faru ba.

**3. Wurudi**

A yi wurudin wannan sura, wato Suratul Ba}arati }afa ]aya, ko she]ani ne ba zai shiga gidan ba da yardarAllah.

Neman [aukaka

{amusunHausa(2006) ya bayyana ma'anar ]aukaka da cewa, }arin girma ko daraja.


[aukaka na nufin samun girma ko daraja a wajen al'umma ko a wani abu.

Bu}atunzucci na iya zama bu}atar da mutum yake da ita na ya kasance ya fifita a kan sauranjama'aya samu kar~uwa. Idan mutum yana da irin wannan bu}atarMalaman sukan ba da gudunmuwa da za ta kai shi ga samun nasarar bu}atar tasa da suka ha]a da:

Ana rubuta wannan Hatimi da Malaman kan bayar, don neman samun ]aukakaga Allah.

1. Hatimi

بسم الله الرحمن الرحيم


بسم الله الرحمن الرحيم

Wannan hatimi yana daga cikin fa'idojin da malaman sukan bayar. Za a rubuta a allo a sha har kwana talatin, sannan a sanya kaninfari, sai mutum ya ri}a sha yana shafawa a fuska. Matu}ar mutum ya juri yi, to kuwa zai sami ]aukaka }warai da kusanci wajen shugaba. Haka kuma, zai zama maganarsa tana da tasiri }warai da gaske cikin jama'a, in Allah Ya so.

**2. Ayoyin {ur'ani**

ورفعناه مكان عليا

A rubuta wannan aya Warafa'anahum Makanan Aliyya, }afa dubu goma sha biyu a sha ha]i da kaucin rimi. Za a sami ]aukaka da yardar Allah.

**3. Wurudi**

يا رافع

A yi wurudin wannan sunan Allah, Ya Rafi'u }afa ]ari uku da hamsin da ]aya, kwana bakwai, za a sami ]aukaka da yardar Allah.


Mallaka

{amusun Hausa (2006) ya bayyana ma'anar mallaka da cewa, kasancewar abu na mutum shi ka]ai ko tare da wani.

Mallaka a nan tana iya kasancewa neman samun tasiri a kan wani miji ne ko mata ko mai gida ko shugaba, don a ri}a sarrafa shi yadda mai mallakar yake bu}ata.

Malaman sukan bayar da taimako domin a mallake mutum, na miji ko mace ga masu zuwa wajensu neman taimako, ga irin taimakon da sukan bayarda ayoyin Al}ur'ani.

1. **Hatimi**



Wannan hatimi ne na Ismillahil A'azam wadda yake san ya yi mallaka, ya rubuta wannan hatimi a gishiri ya zuba a faranti. Ya ja wa]annan ayoyi }afa ]ari da sha ]ai-]ai Ya Allahu, Ya Nurun, Ya Hayyu, Ya Muminun da yardar Allah bu}ata za ta biya.

**2. Ayoyin {ur'ani**

بسم الله الرحمن الرحيم
فإن تولو افقل حسبى اللهلا إلله الاهوعليه توكلت وهورب العرش العظيم
أللهم انت رب حسبي على فلازبنولانة واعطع فلبه وذلله لع أوإلي

Idan ana son ai mallaka, sai a karanta aya }afa ]aya, addu'a }afa]aya, har sau talatin-talatin. Amma a wajen Fulani, sai a fa]i sunan mutumin da ake son a mallake da sunan mamansa, in Allah Ya yarda za a mallake shi.

**3. Wurudi**

بسم الله الرحمن الرحيم
وصلى الله على النبى الكري
قل هو الله احد (1)
اللهم صلى على النبى الكريم (66)
الله اكبر (1)
الله الصمد (1)
اللهم صل على النبى الكريم (66)
الله اكبر (1)
لم يلدولم يولد (1)

اللهم صل على النبى الكريم (66)
الله اكبر (1)
ولم يكنله كعواالحد (1)
اللهم صل على النبى الكريم (66)
الله اكبر (1)

1. Idan ana son a sami mallakar mutum ko rinjaye a kansa, sai a yi Nafila raka'a biyu. A karanta}ulhuwallahu a had }afa ]aya, sai Allahumma salli Ala na Biyyul karim, sau sittin da shida, sai a fa]i sunan wanda ake son a mallaka, sai Allahu akbar sau ]aya. Haka za a yi ta yi akowane sau sittin da shidain Allah Ya yarda za a mallake shi da izinin Allah.


Bu}atun Kasuwanci

Zaruk da wasu, (1987) sun ce, a saya a sayar shi ne, kasuwanci, wato a nan mutum ya fitar da ku]insa ya sayi }adara, sannan wani lokaci ya fitar da wannan }adara ya sayar.

Kasuwanci na nufin a sayi wani abu kaya ne ko abinci ne, don a sayar da shi domin a samu riba.

Malaman Kusfa sukan ba da taimako, don neman sa'a da samun kasuwa, ko kuma wani wuridi da a kan yi, na Allah Ya kawo ciniki da bu]i.

1. **Hatimi**



ومن تيق الله يجعل له مخرجا * ويرزه من حيث لا يحتسب * ومن يتوكل الله فهو حسبه إن الله بالغ امره قد جعل الله لكل شيء قدرا *

A rubuta wannan hatimia allon azurfa sai a yi salati ga Annabi sau dubu ]aya da ]ari da goma sha ]aya. Allah zai bu]a ma mutum kasuwancin shi.

**2. Ayoyin {ur'ani**

بسم الله الرحمن الرحيم و صلى الله على النبي الكريم :-
اللهم فرج عن صاحب هذه التجارة و صنعته و ما يعمل بيده وانه من سليمن وانه بسم الله الرحمن الرحيم:- ألا تعلو علي واتونى مسلمين و رزقنهم من الطيبات وفضلنهم على العلمين اللهم فرج عن صاحب هذه التجارة كما بعث لمحمد صلى الله عليه وسلم وبعث لابى بكران الذين يتلون كتب الله وأقامو الصلوة و أنفقوا مما رزقنهم سر وعلانية يرجون تجارة لن تبور :- فحسبتم أنما خلقنكم عبس و انكم الين لاترجعون :-قل ان كنتم تحبون الله فاتبعون احببكم الله ويغفر لكم والله غفور الرحيم :-واذا راو تجارة أو لهوا انفضو اليها من التجارة والله خير الرزقين.

Wannan maganin samun kasuwa ne, za a rubuta wannan aya a takarda, sai a yi laya a rataye a wurin kasuwancin ko a shago, sannan kuma sai a yi wuridin wannan aya.

**3. Wurudi**

و اذا راو تجررة او لهوا انفضوا اليها التجارة (1)

Sai a yi wuridin wannan }afa arba'in da ]aya(41) sai a karantaYa jami'u}afa ]ari da goma sha hu]u, sannan a shafa. Wannan kasadun ne da yardarAllah.Dukwanda ya tsayu da yi, to kuwakasuwaza ta bu]ejama'a za su dinga zuwa siyayya wajensa.

Binciken ya gano asalin Unguwan Kusfa ta kafane a sanadiyyar zuwan Malam Shitu [an Abdulra'uf kuma ta sami sunanta ne daga Kwasfa, wato magudanar ruwa, binciken ya gano Malam [ibbu a Unguwar Kusfa da irin

littafan [ibbun da suke amfani da su. Har ila yau, binciken ya gano ire-iren taimako na magungunan waraka da Malaman Kusfa ke bayarwa, dangane da fannonin rayuwa mabambanta.

6.1 Shawarwari

Hausawa kan ce "shawara ]aukar ]aki" saboda haka, wannan nazari bayan bayani kan samuwa da ha~akar [ibbu a Unguwan Kusfa da ke Zariya, yana bada shawarwari kamar haka:

i. Duk wani mai neman sanin ilimin magungunan [ibbu, yazo Anguwar Kusfa dake Zariya domin akwai masana wannan fannin da zai samu }arin haske.

ii. Yakamata al'umma su fahimci cewa Anguwar Kusfa, Anguwa ce ta bayar da magunguna da basu sa~awa shari'a ba.

iii. Anguwar Kusfa, cibiya ce ta samun bayani akan ilimin [ibbu, watau bayar da magunguna. Yakamata malaman [ibbun da suke Anguwar su ri}a shiga kafafen ya]a labarai domin ilmantar da al'umma.

iv. Al'umma su daina kallon Anguwan Kusfa a matsayin Anguwa ta malaman [ibbu da Bokaye. Tun farkon Anguwan [ibbu ne Tsibbu ba.

v. Ya kamata Malamn [ibbun da suke Anguwar Kusfa da su ri}a buga littattafai na wayar da jama'a akan amfanin magungunan [ibbu.

**Kammalawa**

Wannan nazari ya tattaunane kan samuwa da ha~akar [ibbu a Unguwar Kusfa da ke cikin garin Zariya. An yi bayanin Unguwar Kusfa da samuwar [ibbu a Unguwar an kawo ha~akar [ibbu da Malaman [ibbu a Kusfa da irin litattafan [ibbun da malaman suke amfani da su wajen tafiyar da harkan [ibbun su, bugu da }ara an bayyana irin magungunan [ibbun da malaman kan bayar nay au da kullum a }arshe aka bayar da shawarwari da kuma kammalwa da manazarta

**JERIN SUNAYEN MALAMAN DA AKA YI HIRA DA SU**

| S/N | SUNA | SHEKARU | RANA | WAJE | LOKACI |
|---|---|---|---|---|---|
| 1. | Malam Suyu]i Abubakar | 45yrs | 15/2/2021 | No 12 Kusfa Zariya | 8:00pm |
| 2 | Malam Abdulra'uf Shehu | 50yrs | 3/8/2022 | No 66 Kusfa Zariya | 9:00am |
| 3 | Malam Adam Sa'id | 62yrs | 6/1/2020 | No 18 Kusfa Zariya | 4:00pm |
| 4 | Malam Yunusa Abubakar | 40yrs | 28/1/2021 | No 30 Kusfa Zariya | 2:00pm |
| 5 | Malam Hussaini [alibi | 65yrs | 5/1/2021 | No 26 Kusfa Zariya | 10:00am |
| 6 | Malam Muhammad Tasi'u | 84yrs | 1/1/2021 | No 11 Kusfa Zariya | 5:00pm |
| 7 | Malam Muntari Tanimu Akibiya | 50yrs | 27/6/2021 | No 75 Kusfa Zariya | 4:00pm |
| 8 | Malam Aliyu [ansidi | 55yrs | 21/5/2020 | No 28 Kusfa Zariya | 10:00am |
| 9 | Malama 'Yar Inna | 76yrs | 1/2/2020 | No 76 Kusfa Zariya | 4:00pm |

**Manazarta**

Adamu, A.T. (1990). "Siddabaru A }asar Hausa". Kundin digiri na biyu. Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Kano: Jami'ar Bayero.

Ahmad, I. A. (1984). "CututtukanCiki da Magungunansu". Kundin digiri na farko. Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Kano: Jami'ar Bayero.

Bunza, A.M. (1990). "Haya}i Fid da Na Kogo: Nazarin Siddabaru Da Sihirin Hausawa". Kundindigiri na biyu, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Kano: Jami'ar Bayero.

Bunza, A.M. (1995). “Magungunan Hausawa A Rubuce: Nazarin Ayyukan Malaman Tsubbu.” Kundin digiri na uku. Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero,Kano.

Bunza, A.M. (1998). “Surkulle”. Mu}alar da aka gabatar a Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Sakkwato:Jami’ar Usmanu [anfodiyo.

CNHN, (2006). *Kamusun Hausa: Kano Jami’ar Bayero*.

Funtuwa, A. 1. da Gusau, S. M. (2010). *Al’adu da [abi’un Hausawa da Fulani*. Kaduna: El-Abbas Printrs and Media.

Garkuwa, B.G. (2007).“Unguwannin Birnin Zariya da Tarihinsu.” Kundin digiri na farko. Sashen NazarinHarsunan Nijeriya. Zaria: Jami’ar Ahmadu Bello.

Maryam, A. (1996). “Mata Da Bu}atun Tsubbu”. Kundin M.A. Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya,Kano: Jami’ar Bayero.

Sani, J. M.(2017). Gudunmawar Malaman Aufa}u Ta Hanyar Magungunan Hausa. Takardar da aka Gabatar A Taron }ara wa Juna Sani a Duniya. A Cibiyar Binciken Harsunan Nijeriya, Fassara da kuma Hikimomin Al’umma ta Jami’ar Bayero, Kano.

Yusuf, B.T. (2002). “Jigo Da Salon Rubutattun Wa}o}in Furu’a Na }arni Na Ashirin”. Kundin Ph.D Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya Sakkwato: Jami’arUsmanu Danfodiyo.

Zaruk, M. da Bello, A. (1987) *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa: Don {ananan Makarantun Sakandare. Littafi NaBiyu*. University Press Ibadan.